# ORGANIZING FOR POWER: JAGORA MAI KUNSHE DA BAYANAI



# Organizing for Power shirin horo ne na duniya wanda ya mayar da hankali kan muhimman batutuwan da suka shafi shirya tsare-tsare.

Shirin horaswarmu na kyauta da ake yi ta yanar gizo wanda an tsara ne don taimaka muku da waɗanda ke kewaye da ku wajen gina shirye-shirye na gangami da ke iya samar da nasarorin da ke sauya alaƙoƙi na iko da kuma rayuwar jama'a.

Daga 2019 zuwa 2025, mun koyar da hanyoyin tsara samun nasara ga sama da mutane 50,000 daga ƙungiyoyi sama da 2,500 cikin ƙasashe sama da 120.

Rubutawa da gyarawa: Clémence Hutin, David Labi, Ethan Earle, Sarah Reader, Lena Wachweger, KB Brower

**Tsarawa da jadawali:** clan—paraná®

@o4p_organizing

organizing4power.org

info@organizing4power.org

# Bayani daga bakin masu gudanar da shirin O4P

An tsara wannan jagorar domin tallafawa aikin tsara shirye-shirye na masu halartar shirye-shiryen O4P. An tsara shi ne ta amfani da yanayin tsarin aikin da aka tsara shirin O4P, wanda yawancinsa wanda ya kafa ƙungiyarmu ce marigayiya Jane McAlevey ce ta rubuta.

Kamar yadda shirin O4P tun asali ya kasance bisa aikin da Jane tayi ne a gwagwarmayar nemawa 'yan ƙwadagon yanci, sannan kuma aka tsara shi musamman don gwagwarmayar 'yan ƙwadagon, haka nan wannan jagoran shima yawancinsa yayi amfani da misalai na tsari daga gamayyar ƙungiyoyin kasuwanci.

Sai dai, kamar yadda O4P ta girma ta zama tsarin horaswa mai faɗin gaske —tana kuma tallafawa ƙoƙarin tsare-tsaren neman cigaba da ya shafi matsaloli da dama — haka shi ma wannan jagoran yana sa ran rugumar kowa da kowa wajen wayar da kai, yayin da zai ci gaba da riƙo da karsashi da kuma hangen nesa wanda ya sa ayyukan Jane, da kuma shirin O4P, su ka kasance masu amfani ga jama'a da yawa.

Yayin da kowanne misali da ke cikinsa ba lallai ya yi tasiri daidai ga duk mai karanta shi ba, mun yarda cewa wannan jagoran zai iya tallafa wa aikin koma waye, a ko ina a duniya, da ke ƙoƙarin tsara shiri ta amfani da dabarun shirye-shiryen Organizing for Power.

**—Ethan Earle da Sarah Reader**

# Abinda Jagoran ya Kunsa


| | |
|---|---|
| **Muhimman Hanyoyin shirya t-shirye** | 6 |
| 1. Tsarawa da Haɗa kan Jama'a | 9 |
| 2. Kungiyoyin da aka Gina Bisa Tsari da Masu Zaɓin Kai | 10 |
| 3. Masu Rinjaye da Marasa Rinjaye | 13 |
| 4. Shugabanni na Gari da 'Yan Gwagwarmaya | 13 |
| **Manyan Hanyoyin Shirya Tsare-Tsare** | 14 |
| 1. Gano Shugabanni Nagari Cikin Tsarinka | 15 |
| 2. Muhimmancin Kalamai | 19 |
| 3. Tsara Tattaunawarka | 24 |
| 4. Gwajin Tsare-tsare | 33 |
| 5. Haɗa Jadawali | 36 |
| 6. Shirya Dabarun Samun Nasara | 38 |
| **Shawara Ga Sabbin Masu Shirya Tsare-tsare** | 43 |

# Masu Arziki Cinye Du ne.

Kaso 1% na masu arzikin duniya sune suka mallaki kusan kashi 50% na dukkan arzikin duniya.

Rabin al'ummar duniya kuwa kusan ba su mallaki komai bane: bai fi kaso 2% ba kacal.

Masu arziki suna mulkar mu ne ta hanyar rarraba kanmu: tsakanin ma'aikaci da ma'aikaci, da tsakanin maƙoci da maƙoci da tsakanin ƙasa da ƙasa.

Domin gina ƙarfin ikon da ake buƙata don sauya wannan yanayin, muna buƙatar ƙungiyoyin ƙwadago masu ƙarfi da ƙungiyoyin ma'aikata.

Waɗannan ƙungiyoyin ba sa ginuwa da kansu; ana buƙatar dabarun aiki da kuma jajircewa. Kuma dabarun shirya tsari ba abu ne da ake haifar mutum da sanin ba, kuma ba a bayyane suke ba. Shirya tsari ƙwarewa ce: dole sai ka koya, ka samu gogewa cikin dabarunka, kuma ba tare da ka daina jarraba gogewarka ba.



# Muhimman Hanyoyin Shirya Tsari

# Masu dukiya suna da kuɗi, amma mu ke da mutane: Babban makamin yin nasararmu shi ne yawan da muke da shi.

Yawan adadi na mutane cikin tsari shi ne ginshiƙin gina iko don samun nasarori masu tasirin da za sauya rayuwar jama'a. Nasarorin ma'aikata a duk faɗin duniya ba kawai suna da muhimmanci don inganta albashi da yanayin aiki ba ne: yin nasara yana tabbatar da samun madafun iko mai dorewa, kuma yana koya wa sauran ma'aikata cewa suna da ikon kawo canji.

Ware kai yana sanyawa mu zama masu rauni. Kafin mu yi nasara, muna buƙatar rinjayen da yake a bayyane, kuma wanda yake da tsari. Dole ne mu samu kaiwa ga mafi rinjayen ma'aikata ko jama'ar al'umma waɗanda ba su riga sun gamsu da cewa ya kamata su kasance tare da mu a cikin gwagwarmayar ba, bayan ga masu fafutukar da suka riga suka yarda da kai.

" Shirya tsari yana ba da damar samun nasara ga rukunin talakawa da ke ci gaba da faɗaɗa, wato taron jama'ar da ba su taɓa shiga gwagwarmayar ba a baya, waɗanda ma ba sa ɗaukar kansu a matsayin masu fafutuka ko kaɗan.

Wani zalunci da kuma keta haƙƙi guda su ne suke zama dalilin tashi tsaye na gaggawa, amma babban burin shi ne mika ikon daga hannun zaɓaɓɓun attajirai zuwa ga mafi rinjayen jama'a, daga waɗanda su ne kaso 1 cikin ɗari zuwa waɗanda su nekaso 99 cikin ɗari.


Bin mutane ɗaya bayan ɗaya yana da mahimmanci a karan kansa, amma babban amfaninsa shi ne zama hanyar shigar da sabbin mutane cikin tsarin kawo canji da kuma tabbatar da cewa sun ci gaba da kasancewa a ciki. Mutane gama gari ne suke taimakawa wajen yin hasashen iko, da tsara dabarun aiki, da kuma cimma mafita. Suna da matuƙar muhimmanci kuma sun san da haƙan. "


— Jane McAlevey, No Shortcuts

# 1. Tsarawa da Haɗa kan Jama'a

Manufar shirya tsari shi ne cigaba da faɗaɗa rukuninka ta amfani da dabarun dagewa wajen tsari ta hanyar jan ra'ayin waɗanda da a halin yanzu ba sa tare da kai.

Tattara mutane yana sanya mutanen da suka riga suka yarda da buƙatunka: ba ya faɗaɗa rukuninka ko gina ƙarfin iko.





| Shirya Tsari | Haɗa Kan Jama'a |
|---|---|
| samar da iko ta hanyar samun rinjaye cikin tsari bayyananne. | yawanci yana da ƙarancin tsari da kuma manufa, tare da sakamakon da suke a rarrabe tare da shan wahala wajen samar da iko mai ɗorewa. |
| Shigo da sabbin mutanen da ba su riga sun amince ba tukunna. | haɗa kawunan jama'an da suka riga suka riga suka amince. |
| Yana amfani da dabarun tsaurara matakan fafutuka: ci gaba da faɗaɗawa da kuma sanya rukuninka cikin aiki. | shan wahala wajen faɗaɗa rukuninka bayan waɗanda suka riga suka amince. |
| ya ta'allaƙa da alaƙar zamantakewa mai ƙarfi. | Yawanci ana siffanta shi da yawan dogaro kacokan a kan kafofin sada zumunta. |
| Mafi rinjayen jama'a ne ke jagorantarsa: babban taron mutane, kungiyoyi masu haɗa kowa da kowa. | yawanci marasa rinjayen ma'aikata ne ke shugabanta tare da 'yan gwagwarmaya. |
| zai iya samar da manyan nasarorin da za a iya karewa kuma a yi gini a kai, kuma ya shafi yiwuwar sauya alaƙoƙi na iko. | yawanci yana samar da nasarori masu wahalar karewa. |

# 2. Kungiyoyin da aka Gina Bisa Tsari da Masu Zaɓin Kai

Domin gina babban rukunai mafiya rinjaye da za su iya samun nasarar kawo sauyi na gaske, muna buƙatar gina tsarinmu a kan yanayin da zai tattaro mutane wuri ɗaya — wato wurare (misali, wuraren aiki, gidajen haya) inda mutane ke rayuwa iri ɗaya (misali albashi mai kyau, arhar kuɗin haya) amma kuma ba lallai ra'ayinsu ya zo ɗaya ba kan matsaloli — saɓanin ƙungiyoyin da ke da zaɓin kansu waɗanda ke tattaro mutane bisa amincewar da tuntuni suke da ita kan wasu al'amura ko wata manufa da ta haɗa su.

| Shirin Jama'ar bisa tsari... | Kamfen na zaɓin kai... |
|---|---|
| ana aiwatar dashi a wuraren da mutane suka taru a inda "tsari" ya zo iri ɗaya, kuma ya kasance ba lallai suna da (ra'ayi) iri ɗaya ba. | ana gane shi ta mutanen da suka shiga wata ƙungiya saboda suna da buri kan manufar ƙungiyar. |
| yana ba ka damar ka duba rukuninka kuma ka sani idan ka cimma rinjaye. | yana da wahala ko ma ba zai taba yiwuwa ba ka samu damar sanin yadda samun rinjaye yake. |
| yana mayar da hankali kan ƙokarin mutanen da (har yanzu) basu riga sun amince da dukkan batutuwa ba. | ya mayar da hankali kan yarjejeniyar da da can akwaita wacce suka haɗu a kai kan batutuwa. |
| yana nufin cigaba da alaƙa da mutanen da ta yiwu basu riga sun samu ra'ayi kan kasancewa a cikin fafutukar ta ka ba. | yana nufin kana ƙarar da mafi yawan lokacinka ne cikin magana da mutanen da sun riga sun amince da kai. |
| Misalai: makarantu, wuraren bauta, gidajen haya, da wuraren aiki. | Misalai: gangami na wata matsala ƙwaya ɗaya rak, gangamin wayar da kai da kafafen sada zumunta (tara mutanen da suka riga suka yarda da kai). |

“Tsarin da aka kafa bisa tsari yana dagewa wajen gina masu rinjaye na masu ra’ayi iri ɗaya waɗanda ta yiwu sun fara ne da ra’ayi kaɗan ko ma babu ra’ayi gabaɗaya na kasancewa a cikin kowacce ƙungiya…

Tsarin mai  zaɓin kai ya dogara ne da matakin haɗa kan jama’a, mahalarta suna da wani ra’ayi ko wani ƙwaƙƙwaran buri da fafutukar.”


– Jane McAlevey, 2016.

# 3. Masu Rinjaye da Marasa Rinjaye

**Abin da za ka iya nasara kai sakamako ne ga irin ƙoƙarinka waje samar da iko.**

Wajibi ne samar da rinjaye mafi yawa don ƙirƙirar rikici ga abokan hamayyarka, ka kuma samu manyan nasarorin da za su sauya rayuwar mutane.





| Masu rinjaye... | Marasa rinjaye... |
| --- | --- |
| yana nufin mutane da yawa sun ɗauki mataki: iko mai yawa! | yana nufin waɗanda dama ake tsammani su ne suke ɗaukar mataki: iko kaɗan. |
| na nuna cewa ikon mu yafi ƙarfi tare da juna: waɗannan matakan zai yi wahala a dannesu. | yana kwatanta wariyar kai da kuma rauni, kuma danne su abu ne mai sauki. |
| Iya yawan masu rinjaye, iya girman damarka ta samun nasarori manya da kuma iya kare abin da aka samu nasara akai. Su ne matakan fafutuka mafi wahala (misali, yajin aiki) wanda ke bukatar gina manyan rukuni mafi rinjaye. | Iya yawan ɗaukar matakanka wanda marasa rinjaye ke yi, iya wahalar samun nasararka, iya ƙanƙantar yadda nasararka take, kuma iya wahalar da za a samu wajen kare abin da aka samu nasara a kai. |

# 4. Shugabanni na Gari da 'Yan Gwagwarmaya

Da yawan fafutukar da ake yi sun dogara ne a kan "'yan gwagwarmaya"— mutanen da suka yarda da kai, suke hallarta, kuma a shirye suke su ɗauki mataki. Amma akwai buƙatar wani ɓangaren wurin samun nasara kan abin da ba a riga an yanke hukunci a kan sa ba da kuma samar rinjaye mai ƙarfi: Wato Shugabannin Nagari. Su ne mafi wahala wajen ganowa da kuma shigowa dasu cikin fafutuka, amma kuma su ne **mabuɗin samun nasara.**





| Shugabanni Nagari... | Yan Gwagwarmaya... |
|---|---|
| suna da tasiri mai yawa a tsarin, amma ba lallai su amince da ra'ayoyi/buƙatunka ba. | yawanci da su ake damawa kuma sun riga sun amince da ra'ayoyi/buƙatunka. |
| suna da mabiya da kuma ikon jan ra'ayin mutane cikin tsarinka. | ba su da mabiya kuma suna shan wahala wajen jan ra'ayin mutanen da ba su yarda dasu ba. |
| yawanci shigowa dasu tsari yafi wahala saboda yanayin tasirin da suke dashi a tsarin. | Yawancin da kansu su ke shigowa, suna aikin sa kai don taimakawa (ko jagorantar) fafutuka. |
| suna da muhimmanci sosai wajen samar da rinjaye. | Suna yin ayyuka masu muhimmanci don ci gaban fafutukar (misali, taimakawa wajen fitar da guraben wuraren aiki). |

# Manyan Hanyoyin Shirya Tsare-Tsare

# 1.


# Gano Shugabanni Nagari Cikin Tsarinka

# Dalilin Da Yasa Suke Da Muhimmanci

Domin samun nasarori masu ma'ana, kana buƙatar samar da rinjaye mai ƙarfi, wanda ya wuce matakin mutanen da aka saba tsammani waɗanda tuni suke ra'ayi ɗaya da kai.

**Shugabanni Nagari su ne suke tara mafi rinjayen jama'a.** Bisa wannan, suna da mabiya kuma suna da tasiri. Su ne mutanen da sauran jama'a ke saurare, kuma suke yin aiki tare da su.

Shugabanni Nagari su ne masu yanke hukuncin ko za ka yi nasara: za su iya jan ra'ayin ɗaukacin sashe, ko ma'aikata, ko wani yanki cikin dare ɗaya. Idan ba ka shigo da Shugabanni Nagari ba, ko oga / mai gida / masu gudanarwar za su yi amfani da



# Gano Shugaba Nagari

Ba lallai Shugaban Nagari ya kasance wanda kake tsammani ba. Yawancin lokaci ba su ne 'yan gwagwarmayar da ke hallarta a kodayaushe ba, ko kuma mutumin da yake da wani babban matsayi bane. Ba lallai ne ya kasance wanda aka zaɓa a matsayin zaɓaɓɓen wakili ba.

- Ba za ka iya horar da mutum ya zamo Shugaba Nagari ba.
- Ba za ka iya gano su daga waje ba.
- Za ka iya gano su ne kaɗai ta hanyar sauraren jama'an da ke cikin tsarin.



## Tambayi mutanen da ke cikin tsarin:


- Waye aka fi girmamawa a nan – kuma me yasa?
- Wajen waye mutane ke tunkara don neman shawara ko taimako?
- Waye yake aiwatar da abubuwa?
- Wane ne ra'ayinsa yafi juya sauran kan abin da su ke yi?

Daga nan ka saurara, kuma ka ci gaba da tambayar "Me yasa"?. Bayan tattaunawa da mutane daban-daban, ainihin Shugaba Nagari zai fara bayyana.

# Tunkarar Shugaba Nagari



Ya kamata a kodayaushe ya kasance sai a ƙarshe za a tunkari Shugabanni Nagari domin su ne mutane mafi muhimmanci da za a shigo da su cikin fafutuka. Ka fara sanin duk abin da za ka iya game da su: abin da suke damuwa da shi, da kuma waɗanda suke girmamawa kuma suka aminta da su. Wannan mataki ne mai matuƙar muhimmanci, kuma kana buƙatar gano mutumin da ya dace da zai tunkaresu.



Rawar da 'yan gwagwarmaya ke takawa na da muhimmanci a nan: za su iya ba ka muhimman bayanai da za su taimaka maka wajen tunkarar Shugaba Nagari (alal misali, abubuwan da ke da muhimmanci garesu da kuma mutanen da suke da kusanci da su).



Shawo kan Shugaba Nagari ya bi bayanka yana da wahala, domin galibi suna iya yin abubuwa ne da kansu su cimma nasara. Sirrin shi ne ka fahimtar da su cewa cimma nasara da gaske na buƙatar yin aiki tare a matsayin masu rinjaye..

# 2.

## Muhimmancin Kalmomi

Yadda kake magana yana da muhimmanci. Yi amfani da harshen da ke mayar da hankali ga mutumin, tare da sanya su a matsayin masu taka rawar gani.

# Yi amfani da “kai” – ba “ni” ko “mu” ba



## Dalili?

Ta yadda wanda kake magana da shi zai fahimci cewa babu abin da zai sauya sai tare da sa **hannunsu.** Wannan yana buƙatar sanya mutumin ya zama shi ne **ƙashin bayan** tattaunawar, ta yadda zai kasance jagoran ‘yantar da kansa ko kuma gwagwarmayarsu na inganta rayuwarsu.

↓

## Ta yaya?

Kada ka ce: “Me □ungiyar/rukunin za su yi?”
Ya fi dacewa ka ce: “Me za ka yi?”

---

Kada ka ce: “Muna buƙatar kowa ya...”
Ya fi dacewa ka ce: “Kai da sauran abokan aikinka/ jama’ar al’umma, da sauransu, za ku iya samun nasara ne kaɗai idan dukkanku...”

---

“Kada ka ji tsoron kiran ma’aikata su gina ƙungiyar kansu.”
— Shawarwari ƙungiyar 1199 ga sabbin masu shirya tsare-tsare

# Kada ka saka ƙungiyar ta ji kamar “a ware” take gefe guda.

## Dalili?

Yin magana game da ƙungiya a matsayin wata rukuni daban, wacce take a ware yana janye nauyin da ya rataya a wuyan kowane mutum.

- Kungiyar ba “wasu mutane” bane ko kuma “mu” ba: su kansu su ne ƙungiyar.
- Babu abin da zai motsa sai su da kansu sun motsa.

“Kungiya ba wajen biyan kuɗi bane a yi maka hidima ba; “Gogayya ce ta faɗi-tashin duka ma’aikata cikin gwagwarmaya.”
— Shawarwarin Kungiyar 1199 ga Sabbin Masu Shirya Tsare-Tsare



# Kada ka ce “mun gode” da ka shigo fafutukar.

## Dalili?

Lokacin da kace “na gode,” kana nuna cewa mutumin ya yi wani abu ne domin ka, ko kuma domin “ƙungiyar.”
Amma ta hanyar shiga wannan fafutukar, **mutane ba alfarma suke yi maka ba — suna ɗaukar nauyin** inganta yanayin aikinsu ne ko rayuwarsu ne da kansu.

## Ta yaya?

Yi murna da matakin da suka ɗauka da kuma amincewa da nauyin da ya rataya a wuyansu:

Kada ka ce: “Na gode da ka sa hannu kan takardar goyon baya.”

Ya fi dacewa ka ce: “Aikinka yayi kyau – wannan ya ƙara tura fafutukarku ta neman ragin kuɗin haya gaba.”

A Lura: Wannan ba yana nufin ba za ka taɓa iya cewa “na gode” ba ne. Idan mutum ya ba ka kofin shayi ko ya riƙe maka ƙofa a lokacin taron ƙungiya, za ka iya gode musu; kawai dai kada ka gode musu don sun halarci taron!

# Yi amfani da harshe mai sauƙin fahimta.

Kar ka yi amfani da kalmomi da aka gajarta ko kalaman da ke rikitar da mutane kamar "CBA" ko "Yarjejeniyar Ciniki ta Bai-ɗaya". Yi magana a kan abubuwan da ke damun mutane kai-tsaye, sannan ka bayyana ainihin abin da ake buƙata: wato samar da IKO.

## Dalili?

Kalmomin da aka gajartasu na iya haifar da ruɗani kuma suna raba kan mutane. Idan mutane ba su fahimci harshen da kake amfani da shi ba, ba za su ji cewa suna da gurbi a cikin tattaunawarku ko fafutukarku ba. Mutanen da za su iya saurararka su ne kawai waɗanda dama sun riga suna goyon bayanka.

## Ta yaya?

Yin amfani da kalmomi masu sauƙi, sannan ka fito da matsalar fili da kuma fito da mafita (cikin haɗin kai) ƙarara.

Kada ka ce: "Lallai ƙungiyar tana buƙatar kowa ya tashi tsaye ya ƙara kwarin gwiwa domin mu samu kariya mafi kyau a cikin wannan yarjejeniyar ta CBA."

Ya fi dacewa ka ce: "Hanya ɗaya tilo da kai da abokan aikinka za ku iya samun irin sauye-sauyen da kuke buƙata a wannan tattaunawar, ita ce idan kai da sauran ma'aikatan wajen aikinka kuka fara samar da haɗin kai da iko a wurin aikin ku, kuma kuka ɗauki matakin farko ta hanyar sa hannu a takardar neman goyon baya.

# 3.

# Tsara Tattaunawarka




# Tsararriyar Tattaunawar Kungiya Cikin Matakai Shida

Shirya tsare-tsare yana buƙatar tattaunawa da mutanen da ba su riga sun amince da kai ba, ko kuma waɗanda ba sa jin cewa sauyi zai iya faruwa.

Tsararriyar Tattaunawar Kungiya tana nuna maka **hanya ne** ta yadda ba za ka ɓata ba. ta sa ka tsaya kan saƙon da kake son isarwa, kuma ta tabbatar ka kai ga duk inda ya kamata cikin rukuninka. Wannan shi ne yadda za ka samu nasarar jan ra'ayin waɗanda basu yanke shawara ba – da kuma samu mafi rinjayen mai ƙarfi – tare da shawo kan Shugabanni Nagari masu wahalar sha'ani don su ɗauki mataki.

Wata ƙa'ida mai kyau lokacin gudanar da Tsararriyar Tattaunawar Kungiya |ita ce ka riƙa yin saurara fiye da maganar da kake yi. Ya kamata ka kasance kana sauraro aƙalla kaso 70% na lokacin tattaunawar.

Kowacce Tsararriyar Tattaunawar Kungiya tana ƙarewa ne da yin **tambaya**. Ka yi magana cikin irin naka salon – amma ka yi amfani da matakai shidan.



# 1. Gabatarwa

**Manufa: Gabatar da kanka da kuma dalilin tattaunawar.**

- Ka yi magana cikin karsashi da ƙwarin gwiwa
- Wane ne kai kuma da abin da ya kawo ka nan



# 2. Gano matsaloli sannan ka motsa rai.

**Manufa:** Gano takamaimaI matsalolin da suka fi damunsu. Kada ka yi tunanin ka riga san matsalolinsu!

- Gano abin da ya ke da muhimmanci garesu a wajen aikin ko gidan.
- Ka yi tambayoyi masu jawabi: idan za ku iya sauya abubuwa uku a wurin aiki, me da me za su zaɓa?
- Bi diddigin tambayoyinka!
- Ka saka musu rai sosai – abubuwa za su iya yin kyau fiye da haka.
- Karkatar da fushinsu zuwa ga mutanen da ke da iko.

Ka gujewa:

- Kada kayi zato.
- Ka yi tambayoyi..
- Ka nuna ka bacin ranka fiye da su ka matsalolinsu.
- Ka yi gaggawa wajen motsa ransu!



Alamomin da ke nuna za ka iya shiga mataki na gaba:

- A zahiri sun nuna fushinsu.
- Suna magana kan rashin adalci.
- Suna tunanin yadda abubuwa za su iya sauyawa.

# 3. Ilimantawa da buri.

Manufa: Bayyana Shirin Cimma Nasara (duba mataki na 6) a matsayin abin da ke da alaƙa kai tsaye da matsalolin da suka ambata. Hanya ɗaya tilo da za su iya samun nasara ita ce ta hanyar samar da iko da yawan jama'a.

**Wannan ne kaɗai matakin da za yi magana fiye da sauraron da za ka yi.**

- Yaɗa burinka kan yadda abubuwa za su iya sauyawa.
- Yi bayanin matakan Shirin Cimma Nasara.
- Alaƙanta matsalolinsu da Shirin Cimma Nasara da yadda ikon da suke da shi a matsayin rukuni guda shi ne mafita ga matsalarsu.
- Bayar da misalai na nasarori.
- Bayyana yadda ƙungiyar/tsarin yake aiki: ma'aikata da yawa ba su sani ba!



# 4. Gabatar da babbar buƙatar tasu.

Manufa: Tambaye su ko a shirye su ke su ɗauki mataki domin magance matsalolin da suka bayyana a Mataki na 2.


- Gabatar da babban buƙatar tasu tare da alaƙanta ta da matsalarsu: "Shin kun shirya ɗaukan matakin farko na cimma nasara a kan ______ ta hanyar yin ________ ?"
- Daina magana. Ka jira duk daɗewar shirun da za a yi – har sai amsar ta fito.



# 5. Rigakafi

Manufa: Tambaye su yaya suke tunanin shugaban zai mayar da martani, sannan ka yi musu gargaɗi game da nau'ikan martanin da ya kamata su yi tsammani. Muna ɗandana musu irin gubar da zata fita daga bakin shugaban ne domin su shirya — tamkar riga-kafi.

- Saurari tsoron da suke da shi tukunna – yaya suke tunanin mutanen da ke da iko za su mayar da martani?
- Bayyana musu cewa duk wani martani na nuna tirjiya da shugaba zai yi, martani ne ga ikon ma'aikata. Shugabanci ya ginu ne a kan iko da nuna isa. Dole ne shugaba yayi turjiya. Ka yi musu shiri ba tare da ka razanar da su ba.
- Karkatar da shakkar ma'aikatan daga ƙungiya zuwa ga shugaba.



# 6. Matakai na gaba

**Manufa:** Zayyana takamaimai aikin da za a yi da kuma bin diddigi.

- Ka buƙaci su yi wani ɗan abu ƙarami. Ka ba su dukkan bayanan da suke buƙata don su yi nasara — wannan za a yi ne domin **ba su ƙwarin gwiwa ne.**
- Alaƙanta aikinsu da Shirin Cimma Nasara.
- Tsara shirin bin diddigi: su wane ne za su yi magana da su, yaushe, kuma ta yaya za ka bi diddiginsu. Kada ka taɓa gamawa ba tare da mataki na gaba ba.



# Magance ƙalubale

Lokacin da ka gabatar da babbar buƙata tasu – galibi mutane suna shiga kokonto. Shakku, karaya, da tsoro abubuwa ne da aka saba gani. “Babu abin da zai taɓa canzawa.” “tsoro nake ji.” “Mene ne amfanin hakan?” Ka mayar da martani ta amfani da wannan dabarar – Amince da damuwarsu, Ba da amsa, Karkatar da magana.

**1. AMINCE DA DAMUWARSU**
Nuna cewa ka fahimcesu – ba tare da nuna rashin ƙwarin guiwarsu shi ne abin da ya kamata ba: “Na fahimceka. Ba abin mamaki ba ne haka kake ji bayan shafe shekaru ana yin banza da kai ba.”

**2. BAYAR DA AMSA (A TAKAICE)**
Bayar da amsa a bayyane, kuma mai ƙarfafa gwiwa. “Abubuwa ba sa canȷawa dare ɗaya – amma babu abin da zai canza idan kai da abokan aikinka ba ku yi komai ba.”

**3. KARKATAR DA MAGANA (ASALIN TUSHEN MATSALAR)**
Yi tambayar da za ta dawo da su kan batun damuwarsu. “Idan da kana da ikon faɗar albarkacin bakinka kan yadda abubuwa su ke tafiya, yaya za ka so ya kasance?”

Sannan ka ci gaba da tattaunawar, ka sake tunzura su, sannan ka sake gabatar da babbar buƙatar tasu a karo na biyu.

Turjiya ba katanga ba ce – ƙofa ce. Dole ne ka sa mutum ya lura da abin da yake tsoro domin ka shawo kansa ka samu rinjayen da kake buƙata.

# 4.


# Gwajin Tsare-tsare

Ananan kamfen don gwada arfin ungiyarku

Gwaje Tsare-tsare suna auna yadda mutanenku suke ba da himma don tantance ƙarfin ƙungiyarku, da kuma sanin lokacin da za ku iya tsananta ayyukanku. Shirinka na Cimma Nasara ya kamata ya haɗa da Gwajin Tsare-tsare masu ƙara tsananta.

**Gwajin Tsare-tsare:**

- Sanya tsarin tuntuɓar kowa da kowa.
- Ka taho da Jadawalin Bango (duba mataki na 5) yayin da kake bin diddigin shigar mutane.
- Taimaka wjaen gwada Shugabanni Nagari (ko sun tattara mutanen sashensu?).
- Gina ƙungiyar.
- Nuna haɗin kai a waje (ga shugabanni) da kuma a ciki (tsakanin ma'aikata/mahalarta).



Ba dukkan Gwajin Tsare-tsare ba ne ayyukan da ake yi a fili ba (misali, bincike), kuma ba dukkan ayyuka ba ne Gwajin Tsare-tsare (idan ba ka bin diddigin halartar mutane)

Don Gwajin Tsare-tsare na fili: burinka a kodyaushe shi ne ka kai ga aƙalla mafi rinjayen mutane a cikin tsarinka.

**Yajin aiki shi ne babban Gwajin Tsari na ƙarshe.** Ana shirya shi ne a matsayin matakin ƙarshe, sa'ar da ka tabbatar ka samu gagarumin rinjayen mutane a cikin tsarinka waɗanda suke shirye don gudanar da gagarumin aikin haɗin kai mai haɗari. Wannan shi ne lokacin da ramuwar gayyar abokin hamayyarku za ta kai ƙololuwa: za su yi ƙoƙarin shuka shakku, da rikici, da raba kai a tsakaninku. Kana buƙatar ka kasance a kololuwar ƙarfinka don samun nasara!

**Misalin matakan tsananta Gwajin Tsare-tsare:**

- Cike takardar bincike (36% na masu zaman gidan haya)
- Sa hannu kan takardar neman goyon baya (51% na masu zaman gidan haya)
- Manna sitikar fafutar jikin akwatin wasiƙunka (64% na masu zaman gidan haya)
- Halartar gangami (72% na masu zaman gidan haya)
- Yajin aiki! (86% na masu zaman gidan haya)

# 5.

# Haɗa Jadawali

Kayan aiki mai sauƙi amma mai tasiri sosai da ake amfani da shi don bin diddigin halartar mutane.


Jadawalin bango na taimaka maka wurin bin diddigin shigar mutane, da fahimtar dangantakar zamantakewa, da kuma tsara taswirar cigaban fafutukarku. Su na da matuƙar muhimmanci musamman wajen gano Shugabanni Nagari.

## Dalili:

- Tattara bayanai waje guda.
- Ganin girman matakin da aka dama da mutane.
- Nuna giɓi cikin halartar mutane.

## Ta yaya:

- Ka jere dukkan ma'aikata a kan babbar takarda. Yana da kyau a yi amfani da takarda ɗaya ga kowane sashe.
- Za ka iya amfani da alƙaluma masu launuka daban-daban, da alamomi, ko sitikoki wajen bayyana halartar mutane cikin Gwajin Tsare-tsare. Wannan yana ba da damar yin jadawalin cikin sirri.You can also organize the Structure Tests listed at the top as columns — allowing you to tick boxes where individuals participated.
- Haka kuma za ka iya tsara Gwajin Tsare-tsaren da aka lissafa a sama a matsayin rukunai — wanda hakan zai ba ka damar yin maki kan inda mutane suka halarta.
- Bi diddigin shigar mutane ta hanyar amfani da launuka daban-daban ga Gwajin Tsare-tsare daban-daban. Tare da amfani da alƙaluma masu launi, da sitikoki, da sauransu, ka nuna: Wane ne ke ɗaukar wanne mataki? Wane ne Shugaba Nagari? Wane ne ke adawa da fafutukar?



- Waɗannan takardu ne masu canjawa waɗanda ma'aikatan da kansu ke amfani da su: sabunta kuma ka yi amfani da Jadawalin bangonka bayan tsararriyar tattaunawar ƙungiya, ko lokacin tarurruka!

# 6.

## Shirya Dabarun Samun Nasara

Fafutuka za ta iya samun manyan nasarori ne kawai lokacin da ka samar da isasshen ikon da zai tankwasa masu yanke shawara su ɗauki mataki. Shirin Samun Nasararka shi ne taswirar da za ka bi don samar da wannan ikon.

Wajibi ne a samar da shi kafin ka ƙaddamar da fafutukar tare da mambobin ƙungiyarka, amma takarda ce mai canjawa wacce za a iya amfani da ita.




# Yadda za ka Tsara Shirin Samun Nasararka.

**1. Bayyana tsarinka.**
Su wa kake tarawa? Mutane nawa ne a cikin tsarinka? A ina suke?

**2. Gano wani bayyanannen al'amari wanda ya shafi kowa sosai, wanda kuma za a iya samun nasara a kansa.**
Wajibi ne al'amarin ya motsa ran mutane mafi rinjaye – kuma ya kasance yana da muhimmancin da zai sa mutane su ɗauki mataki.

**3. Gano waɗanda kake son kaiwa garesu.**
Mutum — ba hukuma ba — wanda yake da ikon ba ka abin da kake bukata.
Ka san abin da suka damu da shi: kuɗi, ko mutuncinsu, ko matsin lamba daga wasu...

**4. Gano abokan haɗin gwiwa**
Nemo wasu ƙungiyoyin da kuka yi tarayya akan buƙatu. ko mutanen da kuke son kaiwa ga, da/ko waɗanda suke da tarin mambobi dayawa jajirtattu.and/or a large base of engaged members.




**5. Shirya tsarin tsananta mataki.**
Jerin Gwajin Tsare-tsare da aka shirya don haɓaka yawan mambobinka da ƙara matsin lamba a tsawon lokaci, wanda zai kai ka ga waɗanda kake son kai wa ga cikin yanayin tsaka-mai-wuya.

# Shirin tsananta mataki mai kyau...




**Yana farawa kaɗan-kaɗan ne:**
Matakan farko = ƙarancin haɗari, halartar mutane dayawa. Waɗannan suna gina ƙwarin gwiwa ne, kuma su ke bayyana ƙarfinka da giɓinanku..
Misali: Koke-koke, bincike, wasiƙun sa hannun tarayya, da bayanan wurin aiki.



**Yana girma ne da kaɗan-kaɗan:**
Kowanne mataki yana cimma ƙarin mutane, yana buƙatar jajircewa mai ɗan haɗari, su ne kuma suke nuna ƙarin iko.
Misali: wuce matakin raba takardun sanarwa, zuwa sanya hannu kan takardun goyon baya da hoto, zuwa kan yin gangami, har zuwa yin yajin aiki.




**Kololuwa cikin rikici:**
Lokacin da za ka iya nuna halarta mai yawan gaske — wato mafi rinjaye sun shirya ɗaukar mataki — a sannan ne kaɗai za ka yi amfani da manyan matakai, waɗanda suka haɗa da yajin aiki, mamaye gine-gine, fitar kowa da kowa daga aiki, ko fuskantar masu iko.



**Bin diddigin waɗanda suka shiga ba tare da ƙaƙƙautawa:**
Kowanne mataki yana gwada tsarinka. Ba za ka matsa zuwa wani babban mataki, mai haɗari ba har sai kana da adadin mutanen da za su iya samun nasara. Manufar tsananta mataki ba kawai fitowa waje bane — matsin lamba ne. Kowanne mataki yana sanar da wanda kake son kaiwa garshi cewar: Ka sasanta yanzu, ko ka fuskanci mataki na gaba.

# Tattara komai waje guda



**1. Yawan Mahalarta:**
Don samar da irin ikon da ake buƙata don samun nasarar sauyin da ka ke so, wajibi ne ka tara masu rinjaye cikin.

**2. Gano Shugaba Nagari:**
Yi bincikenka don gano waɗanda suke da mabiya da tasiri a cikin tsarinka. Su ne mabuɗin gina rukuninka.

**3. Kalmomi Suna da Muhimmanci:**
Kalmomin da kake amfani da su suna da matuƙar muhimmanci. A koyaushe ka bawara halartar mutane fifiko a matsayin babban mabuɗin kawo canji.

**4. Tsararriyar Tattaunawar Kungiya:**
Yi amfani da tsarin tattaunawa don shigowa da Shugabanni Nagari, shawo kan waɗanda ba su yanke shawara ba, fito da hujjojin nuna rashin amincewa, da kuma sa mutane su ɗauki mataki.

**5. Gwajin Tsare-tsare:**
Auna ƙarfin ƙungiyarka da kuma sanin lokacin da ya kamata ka tsananta mataki.

**6. Jadawalin Bango:**
Bin diddigin halartar mutane da fahimtar dangantakar zamantakewa.

**7. Tsari Mai Kyau na Samun Nasara:**
Tsara shirin tsananta mataki don ginawa da kuma bibiyar sa halartar jama'a. Kowane mataki ya kasance yana ƙara tsananta matsala ga wanda kake son kaiwa garesu.

# Iyakokin Amfani

- Za ka iya sake samarwa da yaɗa wasu sassa daga cikin wannan jagoran ga wasu kyauta, amma ba za ka iya sayar da waɗannan ayyukan ga wasu ba.

- Idan ka ɗauki wasu yankuna na wannan jagoran, daure ka ambaci aikin kamar haka, "Bisa takardun horarwar da Organizing for Power ta samar").

- Za mu yi farin cikin samun kowanne irin daftarorin da ka samar bisa amfani da  wannan jagoran. Aika mana da saƙo ta info@organizing4power.org yadda za mu gani kuma mu yaɗa aikinka.

- Ka haɗa da kwafin waɗannan iyakokin amfanin tare da duk wani aiki mai alaƙa da wannan jagoran da ka yaɗa.

# Shawara Ga Sabbin Masu Shirya Tsare-tsare

An ciro jerin ƙasa ne daga tattaunawar auna fahimta na daraktoci da manyan masu tsara tafiyar ƙungiyar ma'aikata ta 1199: Kungiyar Ma'aikatan Lafiya na Kasa, a lokacin taron su na shekara-shekara a 1985. Wannan jerin ya zamo babban jagora ga Jane McAlevey da sauran masu tsara tafiyar ƙungiyoyi da dama da suka bi sawunsu.

1. Kusanci ma'aikata, kasance kusa da ma'aikatan.

2. Sanar da ma'aikata cewa ƙungiyarsu ce sannan ka siffanta hakan.

3. Kar ka yi wa ma'aikata abin da za su iya yi [wa kansu].

4. Kungiya ba wajen biyan kuɗin aiki bane a yi maka hidima ba; Gogayya ce ta faɗi-tashin duka ma'aikata cikin gwagwarmaya..

5. Aikin ƙungiya shi ne taimakon ma'aikata wurin samar da canji mai kyau a rayuwarsu.

6. Ma'aikata tamkar yumɓu suke, ba gilashi ba.

7. Kada ka ji tsoron sa ma'aikata su gina tasu ƙungiyar.

8. Kada ka ji tsoron tunkararsu idan basu yi hakan ba.

## Shawara Ga Sabbin Masu Shirya Tsare-tsare

9. Kar ka ƙarar da lokacinka wurin tara ma'aikatan da suke suka fara tsara kansu, a maimakon haka ka tafi [sashi/tsari] mafi muni.

10. Ma'aikata suna gina ƙungiyoyin kariya na kansu — gano su sannan ka samu goyon bayan shugabanninsu.

11. Fushi yana nan tun kafin zuwanka — karkatar da shi zuwa ga aiki, kada ka dusashar da shi.

12. Fushin da aka karkatar da shi na gina ƙungiya mai ƙarfin gwagwarmaya.

13. Ma'aikata sun san hatsarin, kar ka yi musu ƙarya.

14. Kowane ma'aikaci a kan lokacinsa yake — nuna kuzari, da shauƙi, da gaggawa, da kuma ƙwarin guiwa.

15. Rayuwar ma'aikata cikin danne haƙƙi take, don haka basa buƙatar dannewa haƙƙi daga wajen masu tsara ƙungiya.

16. Masu tsari sun cika surutu. Mafi yawancin abin da kake faɗa mantawa ake yi da shi.

17. Sanar da ma'aikata cewa babu wani tsira bayan ikon da suke da shi na kansu.

18. Ma'aikatan da suka haɗa kai za su iya cin galabar shugaba. Sai ka yi Imani da hakan suma za su iya.

19. Kar ka raina wayon ma'aikata.

20. Za mu yin rashin nasara idan ba mu sa ma'aikata cikin fafutuka ba